# Ra’ayi game da wani

Mahalarta taron za su yi la’ƙari da yanda ake samun bayanai ta intanet da suke taimakawa wajen samar da ra’ayoyin wasu game da su. Za su gano masu sauraron sadarwa daban-daban ta intanet, yin la’ƙari da wane irin bayani suke so ya bayyana a lokacin da wani ya binciko sunansu, sannan su ƙara sani game da hanyoyi da yawa da za a bayar da amsa ga abubuwan intanet da ba sa so.

## Kayayyaki darasi

Me Ya Kamata Ka Yi? Takardar darasi

# Wa Ya San Sirrinka?

## Kashe Na 1

**Sanar da Ɗalibanka**

Wane sirri ne kake da shi game da kanka? Bar wannan sirrin a ranka. Ba ka buƙatar raba wannan sirrin da wani ko kuma rubuta shi.

Yanzu ka amsa waɗannan tambayoyin a ranka — kar ka furta amsoshinka ko kuma ka rubuta su:

1. Mutane nawa ne a wannan ɗakin suka san sirrinka?

2. Mutane nawa ne a unguwarku suka san sirrinka?

3. Mutane nawa ne da ba ka taɓa haɗuwa da su ido da ido ba suka san sirrinka?

Yi tunani idan aka ce za ka rubuta sirrinka a takarda kuma a zaɓi mutum ɗaya a wannan ƙungiyar a ce ya karanta shi. Ga wasu ƙarin tambayoyi a nan — kuma, ka amsa su kawai a ranka, ba a bayyane ba ko kuma a rubuce. Bayan mako ɗaya ya wuce:

1. Mutane nawa ne a wannan ɗakin yanzu za su san sirrinka?

2. Mutane nawa ne a unguwarku yanzu za su san sirrinka?

3. Mutane nawa ne da ba ka taɓa haɗuwa da su ido da ido ba yanzu za su san sirrinka?

## Kashi Na 2

**Sanar da Ɗalibanka**

Kana buƙatar yin tunani game da mutanen da za su iya ganin wani sirri ko kuma wasu bayanai game da kai a matsayin "masu sauraron" wancan bayanin.

Samun ka fahimci masu sauraron da kyau zai iya ƙara taimaka maka wajen samun sauƙin yanke hukunci a kan bayanin da kake samun natsuwa wajen rabawa da kuma abubuwa da ba za ka raba da wasu ba. Mai sauraro ya haɗa da wani mutum ko wata ƙungiya da za ta iya samun damar shiga cikin wani bayani.

Da sababbin fasahohin da ake da su yau, masu sauraro za su iya bunƙasa cikin sauri sosai. Saboda wannan ikon na bunƙasa mai sauraro cikin sauri, yana da

wahala — ko ma ba zai yiwu ba — ka sani ko ka ƙayyade mai sauraron bayananka da ayyukanka na intanet. Duk da yake yana da kyau cewa masu sauraro za su iya bunƙasa cikin sauri a lokacin da kake so ka raba aikinka tare da mutane da yawa, ba shi da kyau idan wannan ya faru da bayanan da kake so ya kasance cikin sirri.

Abun takaici, bayanan sirri — musamman ma bayanan da ke da kunyatarwa — yana yawan nishaɗantar da mutane a lokacin da suka gan shi, saboda haka da zarar irin wannan bayanan sun bayyana a intanet, zai iya zama ƙalubale wajen kula da wanda zai ga wannan abun.

A duk lokacin da ka raba bayanai a intanet (ko da kai tsaye ne tare da mutum ɗaya, kamar a rubuce ko saƙon sirri), ya kamata ka shirya ma yiwuwar zai iya yaɗuwa har ya zarce mai sauraron da ka yi nufin cimma.

## Kashi Na 3

**Tambayi Ɗalibanka**

Yayin da ka aike da matsayin da ka sabunta, hoto, ko wasu bayanan a dandalin sadarwar zamani, su wane ne masu sauraron da kake nufin cimma?

Shin ya dogara ne a kan dandalin sadarwar zamani? Ko wani abun?

**Sanar da Ɗalibanka**

Ya dogara ne a kan saitunan sirrinka da kuma dandalin sadarwar zamanin da ka zaɓa, amma masu sauraronka za su iya haɗuwa da abokanka na kusa / mabiya / abokan da ka haɗu da su, ko kuma su faɗaɗa sosai har su haɗa da duk wani wanda ke yin amfani da wannan dandalin sadarwar zamani, ko duk wanda ya binciko ka a intanet. Amma ko su wane ne suka kasance masu sauraron, za a iya kwafar bayani sannan a aike da shi zuwa wani wurin daban, wasu za su iya ɗaukar hoto / hoton allon abun, ko kuma za a iya raba bayanan ta hanyar haɗuwa da mutumin da firarrakin da aka yi a intanet.

**Tambayi Ɗalibanka**

Wane ne mai sauraron da kake da nufi cimma a lokacin da ka ƙara wani abu a dandalin sadarwar zamani?

Wane ne mai sauraron da kake da nufin cimma a lokacin da, misali, ka yi aike a kan farfajiyar Facebook ɗin wani mutum daban, ko a lokacin da ka ƙara wani abu a asusun dandalin sadarwar zamani wani mutumin (misali., ta hanyar yin jawabi a kan ɗaya daga cikin hotunansu, maƙala su a cikin wani aike ko hoto)?

**Sanar da Ɗalibanka**

Wannan zai dogara ne a naka da kuma nasu saitunan sirrin, amma a kai a kai

abokansu / mabiya / abokan da suka haɗu da su za su ga abubuwan, waɗanda za su haɗa da mutanen da ba ka sani ba — wannan zai iya haɗawa da iyalansu, ko masu gudanarwa ko kuma malamai a makarantarsu.

**Tambayi Ɗalibanka**

Yayin da ka aike da saƙo (misali., saƙon kar ta kwana, imel, saƙon sirri / saƙo kai tsaye a dandalin sadarwar zamani), wa kake da nufin cimma?

**Sanar da Ɗalibanka**

Mai sauraronka shi ne mutumin da kake aika ma, amma ka yi hankali — wasu za su iya ganin shi su ma.

**Tambayi Ɗalibanka**

Yaya saƙonka zai iya cimma wasu mutanen baya ga mutanen da aika ma? [hanyoyi masu yiwuwa sun haɗa da hotuna / hoton allo, aikawa, da rabawa ta hanyar wayar da aka yi da mutumin.]

Ta wasu hanyoyi ne cimma masu sauraro da yawa zai iya yin amfani? [Misalai masu yiwuwa sun haɗa da fatan yaɗa saƙo ga mai sauraro da yawa, tattaro mutane, wayar da kan mutane.]

Ta wasu hanyoyi ne cimma masu sauraro da yawa baya ga waɗanda aka yi nufin cimma zai iya zama matsala? [Rabawa baya ga mai sauraron da ake nufin cimma zai iya sanya ka a cikin matsala, jawo tozarci, ɓata suna.]

Wasu yanayi ne za su zama masu muhimmanci a yayin kasancewa da suna mai kyau a kan intanet? [Misalai masu yiwuwa sun haɗa da makaranta / kwaleji / neman shiga jami'a, neman aiki, da yin sababbin abokai.]

# Binciko Ra’ayin Mutane a Kanka

## Kashe Na 1

**Tattaunawa a Aji**

Zaɓi wani fitaccen mutum (misali., wani daga cikin masana’antar waƙa da / ko fim [fina-finai / TV], fitaccen ɗan siyasa, ɗan kasuwa) wanda mahalarta taron suka sani. Google / nemo sunan su a kan na’urorin bincike a intanet da, tare da mahalarta taron, tantance abubuwan ‘yan kaɗan daga cikin abubuwan da suka taso (ka ɗan nuna majigin sakamakon binciken a kan allo). Haka kuma, ka bincika kasancewar fitaccen mutumin a dandalin sadarwar zamanin. Bayan wasu ‘yan mintuna kana bincikawa, nemi mahalarta taro guda biyu su samar da wata tattaunawa a tsakanin fitaccen mutumin da kuma masoyinsa.

**Tambayi Ɗalibanka**

Shin yaya ________ ke ji wajen haɗuwa da wani wanda yasan bayanai da yawa game da su?

Yaya za su ji idan wannan bayanin ba daidai ba ne?

Mutane nawa ne za su iya samun damar isa ga wannan bayanin game da ________?

Yaya ________ zai iya kula da wane irin bayani ne za a iya samu game da su a intanet?

## Kashi Na 2

**Sanar da Ɗalibanka**

Mutanen da ka haɗu da su za su yi amfani da na’urorin bincike domin su nemo ƙarin bayani game da kai. Abun da za su nemo, mai kyau ko mara kayu, zai yi tasiri a kan abun suke tunani game da kai. Idan kana so ka zama kai ke kula da abun da suke gani game da kai, yana da muhimmanci a gare ka san wane irin bayani ne za su iya gani game da kai.

Waɗannan mutanen sun haɗa da waɗanda za su ɗauke ka aiki a nan gaba / makaranta / jami’an bayar da gurbin karatu a jami’a. Ta yiwu jami’an bayar da gurbin karatu ba za su sanar da masu neman gurbin karatun ba cewa suna ganin abubuwa game da su a intanet da / ko yin amfani da bayanan da suka nemo a intanet domin su taimaka musu wajen yanke hukunci a kan bayar da gurbin karatun.

## Kashi Na 3

**Tattaunawa a Aji**

Shirya maharta taron bibbiyu.

**Sanar da Ɗalibanka**

Samar da abubuwa uku da za ka so ka fito da su a lokacin da wani ya binciko sunanka ta Google / binciko sunanka a intanet. Yaya kake ganin cewa waɗannan abubuwan za su bayyana a sakamakon binciken?

Raba tare da abokin hulɗarka

**Tambayi Ɗalibanka**

Me kuka fito da shi kai da abokin hulɗarka?

Ɗaga hannunka idan ka binciko sunanka / da ka bincika sunanka a intanet. Me ka gani? Wane hoto ya fito? Shin ka iya nemo bayani game da kanka, ko akwai wasu mutane a duniya da suka raba sunanka?

1. Idan suna da sanannen suna, nemi mahalarta taron da su ƙara wani bayani a bincikensu, kamar garin da suke zaune ko sunan makarantarsu.

Za ka iya neman mahalarta taro da su binciko kansu ta Gooogle / binciko sunansu a intanet a lokacin aiwatar da wannan aikin idan akwai kwamfutoci ko na'urorin waya da ke da intanet.

**Tambayi Ɗalibanka**

A yayin da ka binciko sunanka ta Google / binciko sunanka a intanet, tambayi waɗannan tambayoyi guda uku:

1. Mene ne farkon 'yan sakamakon da za a samu?
2. Shin ka gamsu da wannan bayanin?
3. Mene ne sauran sakamakon za su bayar da shawara game da wane ne kai? A matsayin ɗalibi? A matsayin ma'aikaci?

Wane ra'ayi ne wani mutum wanda bai sanka ba zai fitar a loakcin da ya ga waɗannan sakamakon? Wane ra'ayi ne za su iya samu idan suka danna sannan suka karanta bayanan da ke ƙunshe a cikin sakamakon?

# Bayar da Amsa ga Bayani Mai Rikitarwa

## Kashi Na 1

### Tattaunawa a Aji

A Bayar da Me Ya Kamata Ka Yi? Takardar Darasin Mahalarcin Taro. Shirya maharta taron bibbiyu. Nemi mahalarta taron da su tattauna labaran a fallen takarda sannan su fitar da dabaru guda biyu / mafita ga kowane labari sannan su yi tunani game da sakamakon da aiyyukansu za su haifar. Ba su mintuna 15 domin su yi wannan.

### Tambayi Ɗalibanka

Me za ka yi a lokacin da wani ya aike da wani abu game da kai wanda ba ka so da / ko ka ga bai dace ba a cikin wancan abun ba?

Me ya kamata a ka yi tunani a kai kafin ka aike da wani abu game da wani?

# Bayar da Amsa ga Bayanai Marasa Kyau

## Kashi Na 1

**Tambayi Ɗalibanka**

Idan ka samo bayani mara kyau game da kanka a lokacin da ka binciko sunanka a intanet (misali., ta hanyar na'urorin bincike, ko dandalin sadarwar zamani), shin za ka iya yin wani abu a kai?

Mene ne misalan abubuwan da ba ka so wasu su gani?

## Kashi Na 2

**Sanar da Ɗalibanka**

Akwai hanyoyi daban-daban a kan abun da ya kama a yi idan ka haɗu da wani abu game da kanka a intanet wanda ba ka so, wannan ya danganta ne a kan muhallin bayanin da kuma nau'in bayanin, a tsakanin wasu dalilan.

Hanya ta ɗaya ita ce "ƙaryata maganar", wanda ke nufin ka jawo hankali / bayar da ƙarin labari masu kyau game da kanka ta hanyar ƙirƙira da kuma kula da abubuwan da za su nuna ka ta hanyar da ta dace. Za ka iya yin wannan, misali, ta hanyar ƙirƙirar dandalin sadarwar zamani a inda ya dace, fara samar da shafin yanar gizo, ko yin ragista a shafin yanar gizo da sunanka.

Hanya ta biyu ta haɗa da matakai daban-daban da za a cire bayanai marasa kyau. Misali:

1. Idan ka ga abun da ba ka so (misali., hotonka), za ka iya gwada tuntuɓar wanda ya aike da shi kai tsaye (musamman ma a dandalin sadarwar zamani da / ko manhajojin aikawa da saƙonni) ka nemi su cire shi.

2. Dandalin sadarwar zamani da yawa su ma suna samar da wuraren da za a kai ƙarar bayanan da kake ganin suna da ban haushi ko waɗanda ba su bayar da sha'awa; abubuwa (misali., hotuna, bidiyoyi, aike mai ɗauke da rubutu) da ke nuna bayanai maras kyu a kanka / bayanai marasa jawo hankali; ba su kamata su kasance a dandalin ba (misali., wanda ke kunyatarwa, karya doka, ko haramtawa); zai bayyana a matsayin zamba — sannan kuma dandalin zai sake bincika sharuɗɗan aiki da al'adun al'umma.

3. A wasu lokutan, za ka iya samun a tilasta bin doka sannan kuma za ka iya, misali, kai ƙara a kotu, wanda ya danganci hukunci, doka (misali a wasu lokutan yin kutse a cikin sirri ko maganganun ƙarya da suke ɓata sunan wani).

4. Wasu ƙasashe suna da wasu ƙayyadaddun dokokin da ke neman dandalin

sadarwar zamani su cire wasu nau'o'in abubuwan da suka karya doka ta hanyar sanarwa [misali., Dokar Tilasta Bin Dokar Hanyar Sadarwa a Germany].

5. Haka kuma ka lura cewa wasu lokutan ƙoƙarin ragewa / cirewa / gyara abubuwa na iya jawo hankulan mutane a kan shi da gangan.

## Kashi Na 3

**Sanar da Ɗalibanka**

Bugu da ƙari, mutanen da ke zaune a Tarayyar Turai ("EU") suna da "'yancin gogewa," wanda doka ta ba su da aka fi sani da "right to be forgotten" (duk da haka wannan dokar za a sanya ta ko da kuwa za su yi tafiya ko za su bar cikin EU). A ƙarƙashin wannan 'yancin na Kula da Kariyar Bayanai Gaba Ɗaya ("GDPR"), mutanen a cikin EU za su iya neman "masu kula da bayani" da su goge wasu nau'o'in bayanai game da su. ("masu kula da bayanai" kasuwanci ne, mutane, hukumomin gwamnati, da wasu waɗanda ke yanke hukunci game da yanda ake yanke hukunci game da kai.)

Akwai dalilai guda shida da mutane a cikin EU za su iya neman a goge bayanai game da kansu. Kowane ɗaya daga cikin waɗannan dalilan za su iya rufe wasu yanayin. Misali, ɗaya daga cikin dalilan da za a neman cire bayanai zai iya zama cewa an tattara bayanan game da "yara" waɗanda suka yanke shawara daga baya cewa haɗuran raba wannan bayanin yana da kyau sosai. Dalilin gaba ɗaya ne sosai. Zai yiwu akai dalilai da yawa da ba za su ƙurgu ba ga ɗan shekaru-asirin-biyar zai yanke shawara cewa yana so a cire bayanin da ya raba a lokacin da yake ɗan shekara sha shida!

Haka kuma akwai wasu muhimman iyakoki a kan 'yancin goge abubuwa. Akwai wasu dalilai guda biyar da za a ƙi amincewa da buƙatar gogewa. Kamar na dalilan neman goge abubuwa, dalilan ƙin amincewa suna da yawa, wanda ya tattara nau'o'in yanayi da yawa. Za mu yi magana sosai game da wani dalili guda ɗaya mai muhimmanci na ƙin amincewa — domin kare 'yancin yin magana — a cikin 'yan mintuna.

GDPR ɗin ya fara aiki a ranar 25 ga watan Mayu, 2018. Yawan lokacin fara aikin GDPR ɗin, yawan yanda da za mu ƙara sani game da yanda mutane a EU za su yi amfani da 'yancinsu na goge abubuwa da kuma yanda kamfanoni, hukumomin gwamnati da kuma wasu za su bayar da amsa.

# Aiki

## Kashi na Ɗaya

### Aiki

Zaɓi na 1, ga mahalartan da ke da shekaru 13-15:

### Sanar da Ɗalibanka

Yanzu da muka yi magana a kan yanda bayanan da kowa da kowa da ake samu a intanet ke taimakawa wajen samar da ra'ayoyi game da wasu mutane, bari mu sanya abun da muka koyaa aikace.

A cikin mintuna 30 na gaba, ɗaya bayan ɗaya, kasance da waɗannan ayyukan:

1. Zaɓi wani fitaccen mutum (misali., wani daga cikin masana'antar waƙa da / ko fim [fina-finai / TV], fitaccen ɗan siyasa, ɗan kasuwa)

2. Binciko bayanan jama'a da ake da shi game da wannan mutumin a intanet sannan ka yi bayani, a wani gajeren sakin layi, yaya wannan bayanin ya taimaka maka wajen tsara ra'ayinka game da wannan mutumin.

3. Idan za ka iya samarwa wannan mutumin shawarwari guda huɗu dangane da yanda za a iya samun abubuwa daban-daban game da su a intanet (misali., kamar canji a cikin saitunan sirri, canji a tsakanin masu sauraro, canji a cikin abubuwa) da / ko wanda babu shi sam (misali., wanda aka goge, wanda aka cire) don inganta yanda wannan mutumin zai gabatar da kansu / yanda wasu za su kalle shi a intanet, me za su zama?

Zaɓi na 2, ga mahalarta taro da ke da shekaru 16-18:

Yin ikirarin cewa kana zaune a wata ƙasar da ba a da dokar yancin da za a manta da abu. Wasu muhawarori ne guda 2-3 za ka iya yi a matsayin goyon baya ga waccan ƙasar domin ta amince da waccan damar? Haka kuma ka ɗan bayyana abubuwa mafi shahara guda 2-3 da za su ƙaryata mahawarorin dangane da matsayinka.

Lura: Wasu ƙasashen suna ba 'yan ƙasar 'yancin magana, ko 'yancin yin magana a kan ra'ayoyi ba tare da tare da barazana mayar da martani daga ɓangaren gwamnati ba ko haramta yin magana. Yaya kake yin tunani a kan "'yancin goge bayanai" ko "'yancin da za a manta da abu" zai yi aiki a ƙasashen da ke da 'yancin yin magana? Ƙayyade Dokar Kariya Ga Bayanai Gaba ɗaya a Tarayyar Yurai ta bayyana cewa bai kamata a sanya dokar "'yancin goge abu" ba a lokacin da za a cire bayanan da za su hana 'yan ƙasa "'yancin bayyana ra'ayoyinsu da kuma bayani." Shin za ka iya

yin tunani a kan wani yanayin da wani mutum zai nemi a cire bayanan shi na ƙashin kansa, amma mutum na biyu zai kawo hujjar cewa cire wannan bayanin ya karya dokar ‘yancin yin magana (misali., wata ɗaliba ta rubuta wani aike a shafin yanar gizo wanda ke ɗauke da bayanan banza game da wani malami; bayan ɗalibar ta bar ajin malamin, malamin zai nemi a cire bayani saboda bayanin bai dace ba; ɗalibar za ta yi ikirarin ‘yancin yin magana a bayyane a kan abubuwan da ta fuskanta a lokacin karatunta a baya)?

Ba mahalarta taron mintuna 30 domin su kammala aikin.

Wannan kayan karantarwar da Matasa da Kafar Watsa Labarai suka samar a Cibiyar Samar da Intanet &amp ta Berkman Klein; Jama'a a Jami'ar Harvard a ƙarƙashin lasisin Creative Commons Attribution-ShareAlike 4.0 International. Za ka iya yin amfani da wannan, har da yin kwafi da kuma shirya samar da ayyuka, ko kuɗi ko kuma wanda ba na kuɗi ba, kamar yanda ka siffanta. Matasa da Kafar Watsa Labarai a matsayin tushen da suka samar da ayyukan na ainihi da kuma raba wasu ayyukan da za su zo a gaba a ƙarƙashin sharuɗɗa ɗaya. Waɗannan da wasu ƙarin kayayyakin karantarwar su ma akwai su a intanet a Dandalin Kayayyakin Karatu da Rubutun Zamani na Berkman Klein.